# Shin za ka so
# RASUWAR
# Mata masu dauke da JUNA-BIYU?



**GUDUNMAWARKA ZA TA IYA TAIMAKAWA WAJEN CETO RAYUWARSU!**

**GOYI BAYAN KUDIRIN DOKAR JIHAR KANO NA SAMAR WA MATA MASU JUNA-BIYU SAUKI!!**

Acikin mintina goma da za a iya karanta wannan sakwon, Akan samu mace me dauke da juna-biyu ta rasa ranta a wajen haihuwa. Haka kuma daga safe zuwa dare, mata masu dauke da juna-biyu kimanin dari da arba'in da biyar kan rasa rayukansu.

**Duba ka gani: A jihar Kano kawai, mace daya kan rasa ranta a wajen haihuwa a kowane mintina goma, sannan kuma mata dari da arba'in da biyar a kowace rana.**

Wannan labari ba kirkirarsa aka yi ba, ba kuma wasan kwaikwayo ba ne, zance ne na hakika. Tabbas hakan ta faru ga matan aure da ke zaune a karamar hukumar Doguwa, haka ma wasu da ke karamar hukumar Bichi, da wasu matan da suka kasance 'yan'uwa ne ga wasu mutanen da ke karamar hukumar Gwale, da 'ya'yan wasu a karamar hukumar Kumbotso, da abokai ga wasu da ke karamar hukumar Bebeji. Saboda haka, wa ya san abin da zai faru a gobe kuma Wadannan matan fa kan kasance matarka ko 'yar'uwa a gare ka ko 'yarka ko abokiyar mu'amalarka.

Wannan matsala ce da ta shafe ka ta shafe mu, sannan kuma ta shafi dukkan 'yan Jihar Kano.

**Wane goyon baya kungiyar CHRICED ta bayar dagane da magance wannan matsalar?**

Cibiyar Kula da Hakkin Dan'adam Da Wayar Da Kai (CHRICED) na kokarin samar da mafita ga wannan matsala, ta hanyar taimaka wa rayuwar mata a Jihar Kano. Bayan da ta yi duba na tsanaki ga matsalar, sannan ta tattauna da maza da mata a unguwani daban-daban da likitoci da masu aikin jiyya da ungwu-zomomi da gwamnatin Jihar Kano. Hakan ya ba mu damar gabatar da rubutattun bayanai da hujjoji ga majalisar jihar Kano don samar da kudiri da zai taimaka wa rayuwar mata masu juna-biyu ta hanyar samar musu da ingantaccen tsarin kulawa a harkar haihuwa kyauta, don samun raguwar rasuwar mata wurin haihuwa.

**Ta Wacce Hanya Dokar Za Ta Taimaka Wajen Tabbatar Da Hakan?**

1. Ta hanyar sanya gwamnati ta samar da isassun kudi a harkokin lafiya musamman ga mata masu dauke juna-biyu.
2. A karkashin wannan dokar gwamnati za ta gina isassun asibitoci masu inganci na zamani da samar da magunguna da injina na zamani da za su taimaka wajen kulawa da wadannan mata.

3. Samar da isassun likitoci da masu aikin jinya da ungwuzoma da za su kula da wadannan mata, ta hanyar samar musu da kyakkyawan albashi.

4. Dokar za ta taimaka wa mata masu dauke da juna-biyu wajen samun rangwamen kashe kudade wajen kula da lafiyarsu kafin da bayan haihuwa.

5. Sannan gwamnati ta tanadi wuraren horar da unguwar-zoma na gargajiya.

Wadannan dalilan da aka bayyana a sama su ne ake ganin za su taimaka a kawo karshen ko raguwar rasuwar mata a yayin haihuwa a Jihar Kano. Domin ganin tabbatuwar hakan, wannan kungiya ta CHRICED na bukatar gudunmawarka don ganin wannan kudiri ya cimma nasarar zama doka.

**Don Me Muke Neman Goyon Bayanka?**

Gwamnatin Jihar Kano tana da sha'awar hada kai da kungiyar CHRICED don ganin wannan kudiri ya samu karbuwa. Sai dai kuma, ita gwamnati tana da hidindumu masu tarin yawa a gabanta, da suka shafi sha'anin al'umma da kungiyoyi daban-daban. Hakan ya zama dole a gare ka da duk wani mai sha'awar ganin mata sun sami sauki wajen haihuwa da raguwar mace-macensu, ya hada kai da kungiyar CHRICED don ganin gwamnati tabbatar da wannan kudiri, don ya zama doka. **Mun tabbata ba za mu iya cimma nasarar hakan ba, sai da hadin kanka.**

**Me Zai Faru Idan Wannan kudiri Bai Samu Nasarar Zama Doka ba?**

Idan wannan kudiri bai samu nasarar zama doka a Jihar Kano ba, to kuwa mata za su ci gaba da mutuwa a yayin haihuwa.

**Ka sani cewa: A kowane minti daya fa mace daya ce take mutuwa a yayin haihuwa, sannan kuma mata dari da arba'in da biyar suke mutuwa a kowace rana. Haka**



**kuma a wata guda mata dubu hudu da dari uku da hamsin ne suke mutuwa, a shekara guda kuma, dubu hamsin da biyu da dari biyu.**

Idan wannan kudiri bai samu karbuwa don zama doka ba, wata rana matarka ko 'yar'uwarka ko 'yarka ko abokiyar mu'amalarka kan kasance a cikin wannan hadarin.

**Ta Wace Hanya za ka iya Taimakawa?**

1. Za ka iya tuntubar kungiyar CHRICED domin samun lamba ko adireshin sakwan kar- ta-kwana na Gwamna ko wasu daga cikin jigajigan gwamnatin Jihar Kano ko 'yan majalisar Jihar Kano wadanda suke da damar ganin wannan kudiri ya zama doka don kai kuka.

2. Ko a kira wadannan shuwagabanni na al'umma ta hanyar wayar tarho ko sakwon kar-ta-kwana don bayyana musu cewa mun goyi bayan gabatar da wannan kudiri.

3. Za'a iya yiwa abokai da sauran 'yan'uwa na jini maza da mata bayanin wannan doka, sannan a ba su lambobin waya da na sakwon kar-ta-kwana da aka samu daga kungiyar CHRICED don a karfafa musu gwiwar yin roko ga manyan jami'an gwamnatin Jihar Kano ta hanyar wayar tarho ko sakwon kar-ta-kwana don ganin an aiwatar da wannan kudiri ya zama doka.

4. Mu a kungiyar CHRICED za mu yi farin ciki idan ka turo mana sakwo ta wayar tarho kan cewa ka goyi bayan wannan kudiri ya zama doka.

Ta yin wadannan abubuwa za ka gamsu cewa kana yin abin da ya dace don ganin ka zama dan kasa mai cikakken 'yanci, kuma ka bayar da gudunmawa wajen ganin an rage mutuwar mata masu dauke da juna-biyu a yayin haihuwa. **Mai yiwuwa ne ta wannan hanyar ce za ka ceci rayuwar matarka ko 'yar'uwarka ko 'yarka ko abokan mu'amalarka!**

**Sako daga:**
**Cibiyar Kula da Hakkin Dan'adam Da Wayar Da Kai**

**Da Hadin Gwiwar:**
**Miseroer (da ke kasar Jamus)**

MISEREOR
IHR HILFSWERK

**Adireshinmu:** Lamba 46 kan Tititn Lawan Dambazau, kusa da Shoprite (Ado Bayero Mall), Rukunin gidaje da ke Gandun Albasa, a Jihar Kano, Nijeriya
**Lambobin Tarho**: 08032354717/08032547131
**Lambar sakwon kar-ta-kwana**: chricedng@gmail.comYanar-gizo www/chriced.org.ng